gyda" Mikewa tayi tamayar da hijabin sallahn sannan tafito yana zaune a kujerun dasuke jere awajen. Idonta jajur, idonshi akan nata "Meyasameki kikayi kuka?" "Haba kuka saikace yarinya" Tafada tana goge gefen idonta , numfashi yaja "I knw how it hurts aikin dakikeyi, but anma ramlat kekadai na yarda zakimin wannan aikin, don Allah kitaimaka min" Kallonshi take taga yadda maraici azuciyanta tace "Namiji munafiki ne, wata fa yakeso anma dayake yanason taimakonta sai wani langwaba kai yake, toh amiran ta mutu ai saimuga wakuma zaka so, sannan a fili kuma tace "Do not mind WAT R FRNDS FOR" Shiru yayi don yagane metake nufi anma babu yadda zaiyi rarrashinta dai yarinkayi sannan yafice, Yana fita gurin inna yawuce, yagaysheta yayinda tasaka masa albarka, tanuna masa jin dadinta fiyeda yadda yake tunani, abdullahi ne yazo sukadan fice suna gaysawa, yana kara jaddadda masa maganan ramlat, shidai yusuf baice komiba don yasan ramlat, yadaice masa ya gwada luck dinsa Rana bata karya inji bahaushe Ayau zaashiga kotu karan da yusuf yayi na nads takashe masa budurwarsa, yau zaa saurari kara ayi case, don haka mutane dayawa sunzo donjin yazaa kare, musamman dasukaji cewa BARR.FARZAN. ne dakuma BARR. Ramlat, abun na dubawa ne, kowa naji dakanshi. Dukkansu sunyi shigansu na lawyers shigan alfarma, shigan ban girma, a inda Judge dinsu Shuraim shizai yanke hukunci, kotu tacika makil, kowa najira afara case, sun shigo kowa yanemi guri yazauna, benaxiratu ma tana daga gefe, idona guliguli inason kwaso muku rahoto

HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Suna zaune saiga alkali yashiga, gaba daya kotun aka mike yana tafiyan alfarma har ya isa zuwa sit dinshi

sai yazauna. Anfito da nads tana zaune an kunce ankwan hannunta, duk wanda yakaleta sai ya tausaya mata, tadawo abun innalilahi, yace “court clerk call the case” Court clerk yafara bayaninsa “In the case of murder between Yusuf Yarima and Nadiya Dahar Azzam, ill like to call the lawyers starting from the complainant” sai yakoma yazauna Ramlat tamike cikin izza da jin kai, dakuma takama da abun data ke yi, tahau dogon takalmi bawanda zaice mata guntu “my names are Barrister.Ramlat Affan a cousel to the complainant with my learned collegue….” Sai farzan yamike shima wanda sai da yanmatan kotun suka kara kallonshi, yana murmushi yace ” Barrister Farzan Jabir” sannam suka koma suka zauna, kotu tayi tsit hatta jamaan dake ta waje suma tsit sukayi, babu wanda bai hallata gun ba, su inna, abdullahi, gydansu yusuf kaf sunzo, haka gydansu nads, nanatu gidado, mamancy, dayyiba salihu da mrym maleka ma sun gabata, hardasu feena, its a tricycle kowa ya bayyana Anfara handling case inda Barrister Ramlat tanemi alfarma agun kotu da zata fara gabatar da tamboyinta zuwa ga nadiya, kotu tabata dama “Zaki iya gayamun cikakken sunanki?” “Nadiya Azzam Dahar” “Meye alakarki da mamaciyar” “Saurayinmu daya da ita” “Kinkasheta ko baki kasheta ba?” “Ban kasheta ba ganina nakarshe da ita naje mushirya, bata yarda ba” “Shikenan” Nan takara neman alfarman kotu dazata kira shaidanta nafarko wato yusuf, yusuf yafito ya tsaya don a tuhumeshi dafarko ansashi yayi rantsuwan duk abinda zai fada gaskiya ne babu karya, babu fage. Daga bisani ramlat tafara masa tambaya “Zaka iya fada mana cikallen sunanka? Dakuma alakarka da mamaciyar” HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR “Sunana yusuf Yarima, ina mazaunin saurayinta ne, itace macen dana fara so a rayuwata” “To

kana daga cikin masu tuhumar nadiya da kissan amira, ,sannan meye kuma alakar ka da nadiya,ko zaka iya gayamana dalilin dayasa sai ita? Tanada mutane anma itace ka kawo , kake kuma zargi" "Ae, nadiya muna mutunci sosai, don har iyaye,saidai yadda nadauketa daban da yadda tadauken, tadaukeni ne a matsayin matsoyinta. Duk wacce nafara nema sai nadiya taraba mu, ko ta illa ta ta, kokuma tasata tabar gari, donhaka dana fara son amira, nadiya tayi iya kokarinta ganin tarabamu, tasha gayamin cewa zata kashe amira, nakam dauka wasa ne da zafin kishi anma ashe dagaske ne" Ramlat ta gyada kanta cikin gamsuwa sannan tace "ya mai sharia, inada wasu files wanda nadiya da kanta tabawa yusuf, inaso kotu tabani dama namiko" Kotu tabata dama, donhaka ta tattara tabawa court clerk yakuwa mike yamikawa alkali wanda yaduba su daya bayan daya, sannan yace tacigaba, tana kallon nads tace "Shin nadiya maganganun da yusif yafada gaskiya ne?" Cikin sanyin murya nads tace "Haka take magananshi, daidai ne" Nan tayi godiya sannan tace "ina fata kotu zata duba wannan case din da idon basira kamar yadda tasaba, takuma tabbatar dacewa ae lallai nadiya itace tasa ayi kisan amira" takoma tazauna, barrister farzan ne yafito, yana kallon yusuf, kotu tabashi daman yayi tambayarsa dayakesonyi wa yusuf "Malam yusuf kamar yadda kace amira itace farkon wacce kake so, sannan nadiya kuma tana sonka, idan na fahimci maganar kana nufin nadiya tana son maso wani kenan ko?" Yusuf yace "ae hakane" "Ita amiran tana sonka ko bata sonka, sannan kai ko ita wayake bin wani" "Gaskiya amira tana sona fiye da yadda nake tunani,sannan kuma ni nake binta ba ita take bina ba" "Toh amma acikin yanmatan dakace nadiya ta rabaka dasu akwai wacce aka taba cewa ta kashe?

Su wancan din dasuke sonka, duk nadiya tafisune?” “Gaskiya bansan dalilintaba, saboda nadiya nake kafa tsaro wa amira ina ganin kaman zata mata illa,” “Anma kasan kishin mata haka yake, kanason abu dole kayi kishinsa nadiya tana kishinka ne shiyasa tayi haka” Yayi godiya wa kotu yakoma yazauna, su inna dasauran mutanen sunfara murmushi gani sukeyi ai anfara samun nasara ganin cewa farzan bai xurfafa tambayansa, saidai daidaikun lawyern cikin kotun tare da yusuf shikanshi dakuma ramlat didnt find it funny, absolutely sunsan cewa hes up to something, alfarma yanema agun kotu dazai mika diary din nadiya wacce take rubuce rubucenta kullum aciki, tundaga ran haduwarsu da amira ta rubuta, har randa suka rabu na karshe alkali yasa aka karba sannan yace kotu taduba, bata boye komi ba, illa nakarshen shi yajawo hankalin mutane akai inda take cewa “No matter how i hate her, how i dnt want to see her exist she has gone nd left me with a burden i cnt unleash myself, shes a very good person to be with, i have learnt a lesson been with her. May you continue to rest in peace amira. Ill remember you for d rest of my life, nd ill tek kia of d person u wish to cherish foreva, (M sorry bazan samu postn ba sai thursday insha Allah, inada test a skul, but if nasamu sarari zanturo muku insha Allah)
5 HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Court tayi shiru kowa da abinda yake sakawa aransa, masu tausayin nads nayi, masu Allah shi kara nayi, duniya budurwar wawa, nads tadawo abun tausayi, alokacin barr.ramlat ta nemi izinin kotu don gabatar da shaidanta na gaba,kotu tabata dama, inda wata budurwa mai kyau tafito ta tsaya, tayi rantsuwar fadar gaskiyanta sannan aka fara mata tambaya Ramlat tanemi tasan sunanta, dakuma alakanta da nadiya “Sunana hauwa mudi, nadiya kuma

nasanta ne sanadin yusuf, alokacin dana fara soyayya da yusuf gurin aikinmu daya, anma nads ita tajawo nadena aiki hatta zaman bauchi ya gagareni," "Saboda mefa? Metake miki haka?" "Kullum cikin razana ni take, tana barazanan kasheni, saudayawa tasha so ta kadeni acikin mota, wani lokacin kuma har gyda take biyoni tacimin mutunci, dalilin barin aikina kuwa shine nadiya tadauramin sharrin sata a office, bansan ya akayi ba nashiga office naga ana binciken jakana saiga gwal aciki, naji kunya don har kuka nayi kowa yaki yarda dani, bansan ita tayiba saidaga baya takirani awaya tacemin kadan daga aikinta, lakanin sata ba abu mai kyau bane don office dinmu tuni suka fara kaffa kaffa dani ana ganina zaafara tattara kaya, har yanzu illan da nads tamin yana bina, don dazaran wani yafara nemana zaiji batun sata" tana fada tana share hawaye, kotun kowa yafara guna guni, ramlat tayi godiya sannan tace wa nads " shin haka yafaru kokuma baifaruba?" "Yafaru, duk abunda tafada gaskiya ne" "Amma nads tun farkon case alkali ya bukaci you should plea guilty, kinki yarda meyasa kikeson bawa court matsala bayan kinsan ke kika kashe ta? Kinrabata da ranta? Ki amsa laifinki kawai mana" Cikin tsananin bacin rai Farzan yamike dakarfi yace "objection my lord, barrister ramlat is forcing d accuse which is against the law," Alkali ya nemi da ramlat ta dakata inda tanemi afuwa takoma tazauna, farzan yafito yakarewa hauwa mudi kallo sannan yace Kinason yusuf ko bakisonshi?" "Ae, na soshi a lokacin"6️⃣HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR "Da nads tamiki wannan sharrin? Kekuma mekika shirya mata? Mekika aikata mata?" "Kawai fadawa yusuf nayi, yakirata yamata magana a waya,anma batajiba, " Farzan yafito da wani takarda sannam yamikawa court, yace "wannan wasika ce da hauwa ta

turawa nadiya, ina rokon court data karanta wannan wasikan, " Aka karba alokacin hauwa tahada ido da ramlat wacce take mata alamun meye? Idonta yafito guli guli, Wasikar ga abunda tace "Nadiya Azzam Dahar, yakamata kisan duk haukanki, duk yarintarki, duk rashin hankalinki, bazaki taba kamoni ba, banda kirki ko kadan, kindauramin sharrin sata and kina expectn nashareki natafi? Bantafiba, ina kula dake. Sannan zakiga sakamako watarana, zakigane Ruwa bata tsami banza, dankalin hausa ba saan ta bature bane, yellow fool." Court tayi shiru inda barrister farzan yace "wannan shaidam kadai zatasa court tasan cewa nadiya tayi laifi anma batayi kisannan ba, akwai mutanen dasukeson ganin bayanta, ga daya daga ciki, inason kotu taduba tagani" Sannan ya matso kusa da hauwa mudi yace "wasikar taki ce ko baki takiba?" "Hauwa ta girgiza kai sannan tace banawa bane, bantaba mata wasika ba" ramlat wacce ta gane kan maganam tadafe kanta tarufe fuskanta. Shikenan mudi ta dama musu alamari Nadiya kuwa wacce take zaune jin mudi tace bahaka bane yasa tamike tama buga table din gabanta da karfi tana kara wanda yaja hankalin kotu kanta tana cewa "Hauwa y r u lying? F*** ass bitch , ill kill u!!!!!, munafuka marar mutunci" rikota akayi kotu tuni ta hargitse Wayyomu, hauwa mudi is now a suspect
[12/4, 9:15 AM] Adda Bena:7️⃣HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Alkali wato shuraim shi yabuga gudumarsa da karfi wanda yajawo hankalin court gaba daya kowa ya nutsu, inda ya tuhume nadiya da simple offence na distractn masa court, hauwa mudi kuwa fita da ita akayi, ramlat ta kara bawa alkali hakuri sannan ta gabatar da shaidanta wato nanatu gidado, tafito tayi rantsuwa sannan ramlat tamata tambayoyi "Menene cikakken

sunanki dakuma alakarki da wacce ta rasu,?” “Sunana zainab gidado, amira kawatace saboda tun yara muke school daya!,” “Mekika sani dake tsakaninsu da nadiya?” “Tundaga ran haduwarsu har ran mutuwarta nasan komi, nakuma san nadiya bata sonta, nema takeyi ta hallakata, harta text da nadiya take mata da barazanar dauke ranta duk agaba ne.nadiya tayi alkawarin kashe amira a gabana, kuma amira bata amsa mata ba, ana saura kwanaki da mutuwan kuma tazo gida tasami amira, tace mata tanaso su sasanta anma amira bata amince ba, don tana tsoronta kuma tana tunanin wani makircin tashirya, ” “Nagode” sannan tajuya kan alkali tace “Dafatan wannan kotu mai basira da adalci zata dubi wannan alamarin da idon basira tayi adalci,” Takoma tazauna alokacin kuma farzan yafito yana murmushi, nanatu bata kulashiba, illa haushi dayabata, ita yanzu wanda yake kusanci da nadiya ta tsaneshi [12/4, 9:43 AM] Adda Bena: 8 HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Batason abunda zai hadasu, hakan yasa takejin haushin shi; shikuwa tambaya yafara mata “Sannunki hajiya zainab, wato lokacin da nadiya tazo su shirya, kamar yadda kikace tazone kenan cikin sanyi da lumana, meyasa kikace tazo da wani munafurcin, bayan kuma bakisani ba,?” “Abunda nasani kenan, nadiya bata taba zuwa da alheri ba,kullum sharri ne” “Akwai wanda kika sani yake gaba da amira bayan nadiya? “Babu , amira mutum ce mai mutunci tana shiri da kowa batada abokin gaba,” Farzan yayi murmushi sannan yace “anma adan binciken danayi nasamo cewa kin So yusuf” ba itaba hatta mutanen dake gurin saida suka tada surutu, kowa da abunda yake fada , tayi murmushi sannan tace “Sosaima, dani tafara ganin yusuf a hall ana wani training, tun lokacin nafara sonshi,

anma ban bari tasani ba, saboda son da take masa yayi yawa, zan iya hakura nabar mata, tafini sonshi, kuma tun alokacin nabar sonshi din, bankuma kullaceta ba" Farzan yakalli alkali sannan yace "ah gaskiya, kotu ya kamata tadubi wannan shaidar dakyau, itama tanasonshi, sannan kawarta ne, kuma kunsan karin hausa da akecewa makashinka na kasanka, baikamata kotu tadau shedanta da muhimmanci ba, saboda itama yakamata tashiga sahun wanda zaa zarga" inaso kotu tabani dama nakara bincike game da ita da shaida ta biyu, Yakoma yazauna, inda alkali ya amince da bukatunsa, sannan yace zaa dawo da sati uku, meanwhile yanaso a tsare hauwa mudi, don bincike akanta, anan kotu ta watse, nadiya tamike cikin kuka anma haka aka wuce da ita, abdullahi ne yaje gun yusuf don masa godiya alokacin farzan yazo wucewa, yamika musu hannu sannan yace "Yayan amira rgt?" "Ae" "I hope zaka zama shaida don inada dan tambayoyi na" ramlat ne ta katse shi tahanyan cewa " dat depends on me " Yajuyo yana murmushi sannan yace "i see. I just hope you dnt use your emotions on your client, we shall meet
HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Shiru tayi, tabbas yasan da maganan son datakewa yusuf, Allah yasa kar yayi amfani da wannan daman akanta, kowa hanyansa yanufa, yayinda abdullahi yaja inna sukayi gyda, inna mamaki yagagara barinta, duk tunaninta ya kare, ahaka bata daina kuka yar lelenta tarasu, tanacikin tashin hankali, suna isa gyda, abdullahi yayi wanka ya kwara bacci ta kwasheshi, Ramlat tayi wanka tadauko abincinta rike da cokali babu tunanin dabatayiba, tasan duk hujja suna hannunta, amma da alamu akwai abubuwan dake boye dabatasaniba, tana dama cokalin tagagara hadiye wanda ta sa abaki, jitayi anyi sallama,tadago kanta ahankali sannan tamayar, yana tsaye bai

zaunaba yana kare mata kallo, jikinta a sanyaye take. Kuma yasan matsalarta saidai bayason abinda zai dameta ayanzu ko abunda zai hadasu fada, shi damuwanshi abdullahi yakara masa maganan yana sonta, donhaka zama yayi agefen kujeranta, sannan yagyra murya yana cewa “Sannunki da aiki, thnk u soo much nd God bless” Bata amsashiba, itadai tasan cewa tafara regreting abunda tayi, duk iya kokarinta na danne Zuciyanta, kishine yake neman turnuketa, amira dai tamitu anma kishinta na cinta, ga wai nanatu , dat small gel, itace wai take sonshi, wani zuciyar yace mata “saikingama taimakonshi kinrufa masa asiri, yazo yace yanason wata,” dafa kafadarta yayi dasauri tajuyo, “Ina magana kinyi shiru, watz wrong?” Janyeshi tayi ajikinta, tareda cewa “tek note! Niba muharammarka bace” shiru yayi ya janye jiki. Sannan yamike “Ull not regret helping me, and abdullahi yace na isar miki da sakonshi, he has a crush on u” HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Mikewa tayi ta ture plate din gabanta , ranta abace tace “well, tell him tnx,” tafice tabarshi agun. Daki tashiga tazauna ta sha kukanta, tari ya turnuketa, tuni tamike tayi hanyan toilet, jini ne yafara fito mata, hankalinta yatashi, tawanke bakinta tadawo tazauna akam gadon, she just wished , just once in her life yusuf yace yana sonta, bata taba tsanan soyayya irin na yanzu ba, data kasance very close da yusuf, soyayya bata dadi, inhar kai kake kidanka kake rawanka kai kadai, tadauko wayamta tana kallon hotonsa, yusuf yahadu iya namiji, da ace amira na raye, itace zata samu daman aurenshi tunda ita yakeso, anma Allah baiyiba, kuma baida alamun niyyan canjata da wata, soyayyan shi naneman hanata numfashi, Rike da wayan tayi bacci, mahaifiyarta ce tashigo, takalleta, ganin bacci takeyi ta gyra mata kwanciya harzata

juya taga gefen bakinta da jini, nan da nan tagane, arazane tafito tadauko wayanta, likita takira tareda cewa “nikam dr.ciwonnan fa inaga haryanzu wlh” tanayi kaman zatayi kuka, yace “Ramlat tana da taurin kai, tana nema ta hallaka kanta da damuwa, namata magana taki, treatments dinma ba complete takeyiba, don Allah kitaimaka tasamu abunda takeso” Shiru tayi takashe wayan, hawaye nabin idonta, ko kadan bataso tafara case dinnanba, saboda tasan halin yarta, anma tadaure tadanne tace saitayi, meye amfanin farantawa wanda kasan bazai faranta maka ba? Wanda baima san tanayiba, Itadai da ramlat zata yarda ta auri dan uwanta muhd wanda suke kira da Aju, anma taki yarda, aju yayi iya kokarinsa anma ramlat ta kafe itakam sai yusuf
Shikuwa koda yafito daga gidan bai nufi ko inaba sai office dinsa. Gaba daya kanshi tadaure, damuwansa adaure nadiya ko hankalinsa zai kwanta wayansa ce tayi ruri yaduba sannan yaga baigane numbar ba
“Don Allah da yusuf nake magana?” “Ae”
“Ok, toh , maganan rasuwan amira ne, inaso ne nagayamaka wani abu dabaka saniba, akwai kudi da aka saka da sunan amira na miliyan 25 na gadonta, kuma babu kudin yanzu , nagayama ne ko zaka nemo lawyernka kuzo kuji kundin labarin”
[12/8, 9:18 AM] Bee:1️⃣HANNU DAYA
BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR A
Firgice yamike sannan yace “wake magana?”
“Daga company din babanta” “Gani zuwa, text me address” Keyn motanshi yaja, wani horn dayayi saida maigadi yayi saurin budewa, yanakan tafiya yaga msg tashigo masa, yaduba abun mamaki kuma yaga kobi theatre, yadaisan company na old gra, meya kaishi theatre. Nan da nan yacanja akalarsa zuwa kobi theatre da zummar son ganin meya faru, gurin babu haske ko kadan, hasken wayansa yakunna, yaringa dube dube

, takardu yagani a zube, hankerchief yaciro yasa yadauka, hanyan motansa yanufa yashiga ciki yazauna yafara budewa, tabbas gashi account din anbude twenty years back, anasa kudi kowani wata,,da sunan Amira aka bude, wani abun mamaki shine baataba cire ko sisi daga ciki ba, sai kwana hudu daya wuce, yaduba yaga ancire dubu dari, jikinsa na bari yajuya hanyan gyda, ramlat yadauka yakira, baa daukaba don lokacin tana gaban likita, hakan yasa yanufi gyda gun abdullahi da inna don jin bayani, abdullahi yayi mamaki sosai inda yace “Amira ce kadai takeda access da account dinnan, saboda kafin ta mutu dakaina nakirata tayi sighning din takardun suka fita daga hannuna, naje namata applyn atm, ” Yusuf yaja numfashi sannan yace “Definately wanda suka saceta suka kashe su suka cire kudin, ko hala sun tattarata dashi duba dakinta mana” Inna ta girgiza kai sannan tace “anya dakin zai shigu kuwa?, saboda hatta kayan sawanta na wardrobe nabayar komi na ajiye yadda yake, kuje kudubu dai” Dakin suka nufa, sukahau bincike, abun daya matukar basu mamaki shine duk wani personal abu da mutum zaidauka babushi, babu documents din bank, hatta credentials dinta dake ajiye adakin abbansu daya rasu abdullahi yaje yaduba babu!, Tashin hankali!, nan da nan yusuf yasha jinin jikinsa, yakalli inna yace “hajiya, acikin gidannan akwai assasinate, wanda aka hada baki dashi, kuhado kan masu aikinku kaf!, barinje nadawo” Dare yarufa aamma ahaka yadebo sojoji a barrack dirka dirka guda hudu, kafin yazo masu aiki tunda kan mai shara har maigadi, su takwas, yazaunar dasu yafara magana cikin tsigan lallami “Acikinku waye aka bashi kudi. Yaje yakwaso wasu takardu adakin marigayiyan? Da dakin mahaifin?” Kowa tsit yayi hakan yasa yusuf maimaita tambayansa, saidai yaga ko kadan basuda niyyan magana,

hakan yayi magana wa sojojin yace su matso daga kusa, Masu aikinnan sunbugu anma bawanda yayi magana donhaka yace duk gobe police station zaakaisu, jin haka dasauri saudat, wacce take share share tace “inada magana” Kowa hankalinshi yayi kanta, tana zubar da kwalla tace “Bayan rasuwar ranan nashiga dakin naga mutum, kuma tsiffan macece, ina shiga aka rufe idona sannan ahankali akayi magana akan idan nayi ihu ko nagayawa wani zaakasheni nima shiyasa nayi tsit da bakina, kuma abu aka diba, don harda akwati” yusuf a tsaye yamike tareda cewa “nadiyan nan batada kai, wakuma tasamu?, zan kwakulota, duk wanda taturo ai zansani” [12/8, 10:34 AM] Bee:2HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Mikewa yayi a tsaye sannan yace “inna kike ki kwanta, zanje bank din gobe, zasumin bayanin komi agunsu zansamu, sannan wannan wanda yamin text din yanunamin gun, nakira numban akashe shima zanje mtn office subincikomin, abdullahi ne yayi godiya, yarako shi har motansa, yashiga yayinda sojojin ma suka shiga tasu sukayi gaba, Yana isa gyda yarinkabin takardun daya bayan daya,wani matsanancin son amira nashigansa, yayi nadama sosai, nadaman rashin gayamata, nadaman rashin sanar da ita son dayake mata, duk don gudun wannan ranan gashi ranan tasameshi, tashin hankali tamishi yawa, tunda tafadi tamitu bai kwanta yayi baccin sama da awa uku ba, hankalinsa yaki nutsuwa, zama yayi a kofar gyda kafin yayi horn ya sunkuyar dakansa. Yashaa kukansa, (y d fyn guy dey cry now?, ) idonshi tayi jaa maigadi ne yaleko ganin motan dasauri yabude gate. Hakan yasa yakunna motan yashiga ciki. Saidaya kimtsa kansa don kar kannensa sugane halin dayake ciki sannan yanufi cikin gidan, kazrat na zaune tana ganinsa tamike dasauri don karban jakan

dake hannunsa, baiyi maganaba haka itama tabishi. Ta ajiye masa a saman reading table dinsa sannan tajuya zata fita, yana daga zaune akan gado yace “kazrat” Cak ta tsaya, tajuyo sannan takoma tanemi gu agefensa tazauna,don tagane magana yakeson mata, tana balain son yayan nata cikin sanyin murya yafara magana “Kintaba son mutum yadda kowani numfashi saikinji shi aranki?, kintaba son mutum yadda kowani juyin bacci saikin yi tunaninsa, infact bakya iya bacci akanshi?,” Shiru tayi don ta fahimci inda magananshi ta dosa, “Yaya kayi hakuri, duniyan nawa take balle abunda ke cikinta, Allah yajikanta yamata rahama, abu daya zaka iya mata yanzu a matsayin mai sonta kamata addua, don Allah yaya kadena sa damuwa aranka” juyowan dazatayi taga hawaye fal a idonsa abunda bata taba ganiba sai akan amira, lalle yana sonta, toh shima inbandashi yazaayi kanason mutum baka nuna masa, saida batanan zaifara haukan so, itadai lallabashi tayi tamike tafice, ranan kwana tayi tana tunanin hanyan ceto yayan nata, tassn yanzu mata biyu ke sonsa kuma zasu iya taimakonsa, nadiya da ramlat, toh bawan Allahn nan ya tsani nadiya dongani yake ita tayi kisan, alhali ita jikinta na bata ba itabane, akwai boyeyyen alamari a maganan nann, donhaka ramlat ce last option, shima yusuf baiyi bacciba yakwana da fargaban son sanin wayene? He just hope nadiya ce tasa akayi ko itama zata dauwama a prison taji yadda yakeji aransa, Karfe goma nasafe yafice daga gydan,Zuwansa mtn office suka ce saiya hado da yansanda, hakan kuwa yayi , suka masa tracing layi last usage a kobi theatre, sannan registrrn layin na mace ne, itama yar tsohuwa haka, agarin bajoga gombe, nan da nan yusuf yagane cewa karban layi sukayi, yaji haushi donhaka yasallami yan sandan yanufi bank, don dubawa, sunbasa assurance

cewa ae lallai, ancire dubu dari thru bank withdrawal, yabukaci information suma sunki bayarwa, nan yakara hado yan sandan, aka cika files yayi komi, donma yanada dan matsayi ne abun yake zuwa masa da sauki, donhaka suka basu duk abunda suke bukata Date of withdrawal 3rd may Time: 11:34am Self withdrawal , location :abuja, Yace suyi requesting footage din , sunyi requesting anma sunce masa zaikai awa biyu donhaka yajira aturo, gagara zama yayi ya zauna ya tsaya, har aka turo gabadaya suka duba time din dawanda yayi transactions din "Innalilah wainna ilaihi rajiun," Abunda yake furtawa kenan don mamakin ganim waye HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Hannunsa yasa yana nuna screen din, kalmomin bakinsa duk sun kafe yana kokarin furtasa "A-A-AMII-RA" wani gumi yaketo masa, mutumin yakara masa playing don yagani da kyau,Amira ce arayuwan duniya ko hauka yayi bazai manta da fuskar ba, itace, fadi yayi agun, atake suka tallafoshi, yamike agigice yadauko wayansa gumi yana keto masa,hannunsa na rawa yayi dialing numban abdullahi, "Kaaaaaaazzzzzoooo zenith bank, inajiranka yanzunnan" baisaurari mezaice ba yakashe wayan, shikuwa abdullahi mikewa yayi yafito dasauri dama bayada nisa da gun, cikin mintina kadan ya iso, kiran yusuf yayi dasauri yusuf ya amsa tareda masa kwatancen inda yake, yana shigowa yusuf yakirashi yamasa playing yagani, tabbas amirace donkuwa da zata karbi kudin har zoben hannun hagunta yagani, yayi murmushi sannan yace "i knw kana sonta and kana missing dinta. But kazo annemo maka abunda yadade kana replaying,karfa kasami problem fa, don alamun mental sickness ke damunka" Yusuf tsaki yaja, yajawo kan mouse din yamasa zooming date nd time, tareda cewa "duba date and

time,abunnan ko sati baiyiba, donhaka amira tanada rai,kuma fa it says self withdrawal, dakanta tacire kudinnan, common abdullahi dix is reality” Abdullahi yazura masa ido sannan yace “basai nayi dogon surutu ba, dakanka kaga gawan amira, anwanketa sannan ankaita” “No nidai naga gawanta ajini, tunda har fuskanta jinine. For wat she suffered for, anma banganta bayan anmata wanka ba, hey!! Abdullahi dnt tell me u r involve in dix in anyway !” Wani takaici ya gulli abdullahi, duk da shima zufan keto masa take sannan yace “bamu saba wasa dakai ba, i hav nfn to do wit dix, nd blv me not , dix aint my sister” yana fadan haka yafice yabar abdullahi a tsaye, a gigice yakira wayan ramlat, tadauka cikin magagin ciwo anma yadda ya furta mata maganan bakinsa batasan lokacin data mike ta dafa kirji ba, cemata yayi “amira is alive!!” “Wat?” “Yesss!!” “You crazy” “Wateva, yanxu dai help a broda, kizo zenith m waitn for u der” Bai saurari mezatace ba yakashe wayansa HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Suna tsaye suna jira da yan sandan tashigo cikin gurin sanye takeda abaya, doguwa , fuskanta na nuna alamun tsoro, dasauri yusuf yakunna mata tagani, batasan lokacin data zauna akan kujeran ba, tsantsan rikicewa, gumi yafito mata, takalli yusuf wanda bakinshi har wuya , aranta tace “dix person must be crazy!, antaba mutuwa aka dawone?” “Yhto ramlat kinyadda?” “No banyarda ba, mai kama da itane” “Bangane mai kama da itaba. How can mai kama da ita zata zama tana usn account dinta” Shiru tayi, its a food for thought, duk basiranta tafiya yayi, kallon mutumin tayi tareda cewa “can we have a copy plx?” Saidata sighing takardu hukuma suka sa hannu, donma suna da karfine, da zaibasu wahalar shaani, tadauka suka fito, shidai murmushi yakeyi, can yagagara hakura yace “zanje abuja yau”

Juyowa tayi takalleshi tareda cewa, afadin abuja ta ina zaka fara ganinta? Do u knw dat u r falling into a trap?, someone might do dix to hurt u" "Koma meye, ill be going , " bata saurareshiba, takunna motarta shima kunna nasa yayi kowa yayi gaba, gabanta sai tsananta fadi yake, yusuf gidan inna yawuce yasamu batanan donhaka yanufi asibiti, yaci saa bata da aiki sosai, donhaka ya isa gunta suka zauna, ya gyra murya sannan yace "Inna maganan kudin danaga ancire a bank, naje bank nabukaci sumin bayani naga details, toh kuma abunda yafaru shine sun nunamin videon wanda yakarbi kudin" Tazaro ido tareda cewa "yan fashi ne ko?" Ya girgiza kai tareda cewa "Inna, amira ce, takarbi kudin" Batagane meyake nufi ba, saidaya kara maimaita mata Sannan tace "Bangane wacce amira ba" "Amira dai, amiran gydannan" Tayi murmushi tareda cewa, "Yusuf kaga kasa damuwa aranka gashi har kafara gane gane," "Wlh inna lafiyata lao, amira nagani, amiranki, itace, bata mutuba" Inna ta girgiza kai donta fara tsorata tace "kamanta nina mata wanka kafin akaita?, yata nayiwa wanka , kuma baa taba mutuwa andawo ba" Yayi shiru don yaga bazata yatda dashi ba sannan yace "barin nuna miki kiga" Flash yaciro a aljihunsa, yadauko laptop dayagani akan table din office din, yajona, yasa mata play, sannan yaja baya ya tsaya Idonta kur akai daga farko har karshe. Idonta tuni yaciko da ruwa, tana cewa "ba amira bane, wannan ba amira bane, amirana fa tamutu, gizau ne kawai, innalilahi wainna ilaihi rajiun," fadi tayi a kasa

[12/11, 8:40 AM] Benaxir Omar: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Dasauri yanemo agaji aka farkar da ita, wayansa yasa yakira abdullahi. Cikin mintuna kadan ya bayyana a asibitin yana shigowa alokacin yusuf ya tallabo inna

wacce suka bata bedrest, dasauri ya isa gareta sannan yagaydata da jikin, juyowan dazaiyi yatsaya cak yana kallon yusuf. Wanda ke kokarin bayanin meya faru, abdullahi yasa hannu yatareshi alamun yayi shiru sannan yace “do u knw wat? I dnt get it, kazo kana dagawa mahaifiyata hankali, kasan cewa fa da hannunta tayi wanka wa amira, karamin hauka ne ke damunka ko meye? Kataba ganin mamaci yadawo, its high time u respect urself plx!,” Yusuf yayi murmushi sannan yace “inna kiyi hakuri, but tunanina wannan abun farin cikine shiyasa nagayamiki, anma tunda baa yarda ba, nizance nemanta, kuma zansamota, kuma zan aureta!” Inna dasauri tace “tsaya” ya tsaya donjin mezatace “kayi hkr, Allah fargaba ne yacikani, babu maison yaga amira da ranta irina, donAllah duk abunda ke faruwa kasanar dani, abdullahi kozaka je ne?” “Inje ina inna, bayan nasan ta mutu. Ba inda zanje, kema yarda kikayi dashi kawai, saiya dawo Ify Shidai yusuf yana mamakin hali irinna abdullahi baka gane alkiblansa, if not bcox ciki daya suka fito dayasashi acikin black list yan hassadan amira, Gida yanufa yahau tattara kaya, yana fitowa yaga mammy yayi murmushi sannan yace “zanje aiki abuja” “Saikuma yaushe?” “Saikunganni kawai” Fitowanshi kazrat tabiyoshi, “yaya kayi hakuri kana kula barr.ramlat” “Ita tace bana kulata?” “A a, ni nalura, kaga rashin amira ne yahawo haka” Murmushi yayi sannan yariko kumatunta yace “dont worry little sis, zandawo miki da labari mai dadi” Jan motan yayi dakarfinsa, sai abuja, Yana shiga yafara tunanin ina zaije, gidanshi yanufa wanda ke lugbe, yayi parking yashiga ya ajiye kayansa. Gidan tayi kura donhaka wayansa yadauka yaddanna wa abokinsa faruk waya, tareda cewa yataho da mai aikinsa, aikuwa saigasu sunzo, ta gyra gydan tsaf, shikuna yayi wanka suka

kinkima mota sukayi waje, [12/11, 8:56 AM] Benaxir Omar: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Yana rike da stiyerin mota,anma ranshi na tunanin ina zaifara zuwa, duk fadin abuja ina zaije da sunan nemanta, dafarko tunaninsa shine wacce irin mutum ce amira, yasanta da son zaman gyda kaman me, batason fita, kuma zuwa wurin shakatawa ba idea dinta bane, but yasan tana balain son shiga kasuwa, aikuwa saidayafara tundaga lugbe, harsu wuse market, yayi su gwagwalada, duba agogon dazasuyi karfe goma, donhaka yaroki faruk dasu kwana agydanshi, aikuwa hakan sukayi baiyi bacciba, anma faruk kam harda gwarti, map din abuja yanemo, yanata dube dubenshi, dole nema yajesu manyan shaguna washegari a mota suka karya, karfe sha daya suka nufi shoprite, sai next, sunyi hanyan grandsquare faruk yace “waini tsaya inmunje nan sai ina?” “Sai sahad” “You must to be stupid, ji yadda kake yawo damu, daga grandsquare kadawo damu sahad, wani irin baya ne haka, ni da Allah muje bank din,” Zenith bank sukaje, sukayi confirming tape din, tabbas itane, kuma self withdrawal, which means babu photocopy dinta, ita ce dakanta takarbi kudin, Numbansa yabayar wa managern incase ko zaa sami wani trace, harsun fito managern yakirasu tareda cewa “tunda withdrawal ne, y not kuyi stickn da nan bank din, intana gari definately zata dawo nan din” Faruk ne ya amince atake, donshi yawahala sosai, hakan kuwa tafaru, satinsu uku ajere kullum saisunzo dasafe har arufe bank sunagun, wataran yusuf shikadai ke zuwa faruk nazuwa gun aiki, haryafara hakura, don yafara tunanin komawa bauchi kawai, duk da tsananta adduanshi daya keyi, ana gobe zaitafi bauchi yazauna a reception din bank din wanda harsun saba sosai dasu, wasukam ma sundauka staff ne, Karan takalminta ne yajanyo hankalin daukakan

mutanen dake cikin bank din, tana sanye da abaya, baka, tayi daurin turban, tayi kyau sosai, yakalleta gabanshi yafadi kaman yajuya da gudu anma yayita maza yanufeta sannan yace " AA–AMIRA" Cak ta tsaya daga rubutun datakeyi akam withdrawal slip dinta, hannunta yafara rawa, biron yafado kasa, cikin zakuwa ya fizgota
[12/12, 10:12 AM] Benaxir Omar:
HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Idonta manya manya tadire akansa, wani nutsuwa yaji yasauko masa, fizgotan dayayi rungumota yayi, tuni hankalin kowa yayi kansu, kowa yayi jigum tundaga masu layin saka kudi, har gurin masu laying complain, rungumar dayayi mata damkota yayi dakarfinsa, irin wanda uwa taga danta da baya duniya tunda jimawa, shikanshi yamanta cewa ashefa ta haramta agareshi, haramun ne agareshi yataba wani gaba na jikinta, anma inas yaukam yamanta,Ya matseta don gani yake zata gudu masa. Hawaye na bin layin idonsa, sunfi minti biyar ahaka, batayi magana ba, sannan batayi resistn ba, yasaketa sannan yakare mata kallo, tabbas itace, ba mafarki yakeyiba, hannunsa ya laluma a aljihu yakira faruk tare da cemasa yayi saurin zuwa ko yatafi yabarshi,
Mutanen bank kuwa juyawa yayi yana wage hakori tareda cewa "y'all should jubilate with me, i found my lost wife, we all thought shes dead, " Wani inyamuri daga gefe ya matso kusa tareda cewa "congrats my frnd, you luk cute together" Kowadai natofa albarkacin bakinsa, hannunta yajawo suka fito tana tsaye, yabude mata mota tashiga, anma ta tsaya. Kallonta yayi alokacin nutsuwa tazo masa nacewa ashefa tunda suka hadu batayi magana ba, yace "amira akwai matsala ne?, ko baki ganeni bane?" Hawaye na bin gefen idonta tace "babu" Yadauko hankerchief a aljihunta sannan yashare mata ido, yashigar

da ita motar yazauna [12/12, 10:39 AM] Benaxir Omar: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Taana zaune kanta akasa, wayarsa yadauka yakira ramlat tana kallonsa, yana cewa ga amira ya samu, anma shes not d lively amira he knws, tayi jim sannan tace “kafadawa yan gydansu?” “A a, am planning to” “Karkafadawa kowa, keep her, nd bring her back silently, accomodate her, feed her, nd let us see wat will happen,nadiya is not involve in any of these, i think mujanye karan, on my investigation list na jiya, abdullahi is my first suspect,” Mikewa yayi acikin motan yafice don kartaji maganan, Saida yabar gefen motan sannan yace “Meya faru” “Abdullahi ne yajawo komi, nd it seems ba amira ce kadai ba, dey r identical twins, dax y dakacemin kaganta kuma itane banma musu ba, subiyu ne, but kaman ita kanta uwar batasan subiyu bane, right from birth aka rabasu. Toh kaga wannan dogon zance ne, u have to come back as soon as possible,” Numfashinsa dakyar yake fita, yakashe wayan sannan yajuyo, bata cikin motan , tuni yanemi kwanciyan hankali yarasa yafara dube dube. Can yaganta acikin wata matrix, baka, tana zaune, gun yanufa tareda cewa “Motarki kenan, kiyi driving zanbiki abaya, kokuma bar motan nawa anan muje tare karki subucemin” Shiga yayi ta tuka su har maitama, wani kaftareren gida ta shiga gates din dakansu suka budu, tawuce first gate. Tanufi second gate, nanma taje tayi parking gun motoccin, sannan tafito, all dix while cikansa batace masaba, Fitowansu kenan sukayi hanyar shiga gydan, falon gydan tashiga, komai coffee colour, shikanshi yasan wannan gida, sunanshi gida, zama yayi itakuma ta haura sama, can saigata tasauko da wani saurayi, shikam ganin farko yazata balarabe ne, irin bakaken larabawan nan, yamike suka gaysa sannan

yakoma yazauna, sunzauna alokacin yusuf yagyra mirya sannan yaace “Naga amira ne, shine nabiyota, mundade muna nemanta, kowa yazata ta mutu” Bakin balaraben, wanda gashin kanshi ta kwanto luff akansa yace “wacce amira? Ko kana nufin ummi? Awh. Gaskiya its a long story, but tunda kazo alhamdulilah komi yazo cikin sauki, dama har munshirya aurenmu nxt month” Wani kwarewa da yusuf yayi idonshi awaje yace “wayedin? Amiran? Toh matar aurece!, kasan kuwa aure ya haramta ko!,” baitaba shiga wannan yanayin ba, takaleshi wanda tunda suka fara maganan batace komi ba, sannan tace “Bangane matar aureba, wen aka dauramin aure?, last i knew ko saurayi bandashi, ” “Amira nidin fa?” ‘Ta ina kaidin, akwai randa kataba furtamin so ne?, kataba? If kataba den kazama saurayina, you can talk but not wen uve neva tried” Tunda yake arayuwansa baitaba nadaman rashin furta mata kalmominsa irin na yauba, yamazaayi ne wani kato daga sama yazo yace aure, toh zaman lfy taci gidansu!, wata babbar mata ce ta sauko , kana ganin halittarta kasan cewa mahaifiyar balaraben ne!

[12/14, 11:07 AM] Benaxir Omar:

HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR takalli balareben sannan tace “man haza? Fi mushkila awh mafish?”(waye wannan? Akwai matsala ne ko babu?). Shidai yusuf yasan yanajin larabci, hakan ya tabbatar masa da larabcin yare takeyi. Tafdijam aina itakuma amira ta nemosu, bai idar da tunaninsa ba balaraben yamayar mata da amsa “Mafish, huwa aiz ummi; huwa yuhibbuha (babu, ummi yake nema, yana sonta), Gyran murya yusuf yayi anan taxauna tadaga mai hannu tareda cewa “Sannu sannu, sannu ko, barka!” Bata iya hausaba, abunda ya ayyana aransa kenan, don kame kame takeyi, amira ce taje gefenta

cikin harshen larabci taketa mata magana, larabcinsa baiyi zurfi ba donhaka bai fahimci bayaninta ba, saidata gama sannan bakin balaraben yace “By the way sunana Imran,asalina dan kuwait ne, zama yakawomu nan saboda aikin mahaifina, nikuma shine nakarasa makaranta na anan, wannan kuma mamana ne, batajin hausa sosai, gwara turanci, ” Yusuf ya gyada kai sannan yace “bawannan bane damuwana, nazo daukanta ne nakaita gydansu daga inda tafito” Yayi murmushi sannan yace “toh ai gatanan, saitabaka amsa” Amira kif tabata rai tahade rai wanda baitaba gani tayiba sannan tace ba inda zataje, yayi mamaki sosai juyin duniya taki kulashi, hakan yasa imran yajanyeshi suka fice, bayanin duniya yusuf yaroki imran yamasa akan yadda yahadu da amira yaki, acewarsa amira tahana, Gashi bayason kiran inna, yatuna abunda ramlat tafada masa. Faruk yanemo suka tsaya akofar gydan jira suke tafito su tareta anma kim taki fitowa, Kwanansa uku ajere yanason tafito sumata magana, amira taki fitowa gashi saura kwana shida akoma kotu, dole tayi collaborating saboda susamu su janye kara, don shi jikinsa nabasa amira ce tunda hartaganeshi tace baitaba furta mata kalman so ba, yayinda ramlat tace zai iya yiwuwa ba amira bace, twin sistern ta ne, damuwan shine su rikota komi zaixo dasauki anma baiwar Allahn nan taki futuk tafito Rana tahudu suna gefe a mota , sukaga tafito dasauri yabita. Gudu take kaman zata tashi sama anma haka yabita, bai bartaba itakuwa datagane ana binta saitafara canja hanya
[12/14, 12:59 PM] Benaxir Omar:
HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Bin ta yayi ganin zasu kureta yasa takara gudu, dasauri yasha gabanta wanda yasa tayi mummunan tsayawa, itakanta ta zata tamutu, gabanta

yayi mummunan faduwa, dasauri yafito har ya nufa kanta, bata dago ba ya bude kofan, a tsorace takalleshi idonta yaciko da hawaye , yacirota yaciro mukullin motan sannan yarufe, fizganta yayi yanufi motarsa da ita, faruq na gaba wajen tukawa yabude gidan baya yacusata, sannan yashiga yarufo, tana cewa "mota na fa" bai kulataba haka suka wuce, can hanyar fita agari suka nufa da ita, itakam tarasa mezatace , hanyan bauchi suka nufa, dataga a zahiri bauchi zai nufa da ita tafara kuka, kokari yayi yadanne ransa donkar tagane yana tausayinta, kuka take sosai bawanda yakulata, can dai faruq yaja wawan birki tareda cewa "meye matsalar ki?" "Kuyi hakuri ku mayar dani, don Allah karku maidani bauchi, wallah zaa kasheni nima yadda aka kashe yaruwata!" Shiru sukayi musamman yusuf da yarasa yazaiyi daransa yace "duk lokacin dakika shirya bani labarin meya faru, meya sameki, sannan ta ina kuka zama biyu aka kashe daya, anan zanbarki!, kifadamin wadannan larabawan daga ina kika samosu" Tayi shiru can tace, zanfada muku, kuyi hakuri mukoma don girman Allah" "Bazai motsa anan ba, harsai kinfadamin komi" Tayi shiru kanta a kasa sannan tace "Tun some months back, yayah yazo gida da files yace nayi sighining na kudi ne, danayi agefe dana karanta naga Bayanin mutane uku ne aka kasa, 50% saikuma 25% guda biyu, nadai san nikadai ce mace daga ni sai yayah, toh yayi saurin karba don alokacin har matsifa yamin basai nakaranta ba, sighning kawai zanyi na miko mishi, dana mika mishi, naje nasamu kawata mrym maleka dama tana karanta economies natambayeta ko zata iya min bayani akan yadda zaa raba mana kudin mubiyu, nafada mata total dinshi, tamin bayani cewa tunda shi namiji ne akalla zai dau 75% ni nadau 25%, nazauna nafara bincikena aboye, ta office dinsu yaya nabi, dafarko nagane mu

uku ne, saidai bansan dayan waye ba, nayi kokarin nagane nagagara ganewa, saida ranan dare dare naje office din nafitar da takardun daya bayan daya, naga ta ukun sunanta adiya, certificate of birth dinmu mu biyu, ga kuma muna kama, komi ya tsayamin, naciresu zanfito dasu, don na nunawa inna dasafe, harna fita naga wani yana bina, dasauri nadau mota nadawo, maigadi yabudemin nashigo, na so gayawa inna anma saboda wasu dalilai nakasa, harna kwanta banyi bacci ba inajira safiya tayi, inna tatashen azatonta nayi bacci tace narufo kofa, natashi narufe, Can dare naji anbuga kofan azatona inna ne, sai nabude, ina budewa naga yayah dawani baki a gefenshi, sukasamin abu a hanci, nan nafita hayyacina

[12/15, 10:58 AM] Benaxir Omar:
HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Shidai yusuf yana mamaki, abun duniya ta isheshi, duk ya tsorata, tacigaba da bayani yayinda suke sauraronta "Bansan takamaiman inda suka kainiba, farkawa nayi naganni a guri mai duhu, kuma mubiyu, dafarko dana ganta na tsorata saboda duk halittan jikina babu wanda batadashi, if not saboda ba madubi bane agun, sannan kayan jikinmu ba daya ba, da zan iya cewa lallai ni ne sak, tana kuka itama duk jikinta kwarzane, da jini gashinta yazubo, alamun tasha tsantsan wahala, muna zaune dukkanmu basu kuncemu ba, anma suna tsaye daga waje suna gadi, takalleni itama alamun tsoro sannan tace "ashe kema baki tsira dagaa gun azzalumin nan ba, bausi hadawa dakeba, meyasa kika fara bincike, kika shiga hurumin daba nakiba," nadai yi tsit ina kallonta, don ban fahimci metake fadiba, saidaga baya take sanar dani, yanda abdullahi ya kwakulota, tace ita agydan marayu ta tashi saboda suncema shi yakaita, hakan yasa shiya

karbota, kuma daya karbota yamata barazana da ta sighning takardu taki yarda, hakan yasashi cewa zai kasheta, ni don nayi nawa yayi niyyan barina, anma binciken danahau yi shiyasa yahado hardani akawo, munrasa yazamuyi don neman hanyan guduwa muke, cikin saa tacemin akwai karamin wuka ajikinta tadauka ne lokacin da ya ajiyeta awani gida na wata uku, matsowa mukayi daf da juna, najuya tabaya hannuna nasa tacikin jikinta inda ta cusa, wanda saidanayi mamakin baiji mata ciwo ba, koda yake karami ne sosai, bayan naciro naringa zugawa. Har nayanke igiyan nawa, namike don itama na cire mata, nacire saidai ta gagara tashi, don mummunan illan dasuka mata, nayi nayi tagagara hakan yasa cikin hawaye tace naje, kuma nadau mata fansar mutuwarta, ganin su nayi zasu shigo hakan yasa na labe, naji suna cewa zasu kira inna don su tsoratata kamar yadda yahh abdullahi yace suyi, nayi mamaki kwarai hawaye na bin idona suna shigewa na fantama da gudu, bakin titi na tsaya, ina mika hannu basuda niyyan tsayawa, hakan yasa na tsaya cak a tsakiyan titin wanda drivern yaja birki, yafito yana matsifa da turanci, ban saurareshi ba nabude motan nashiga gidan baya na kwanta luf, kaman yagane menake nufi hakan yasa yashiga yaja yanamin matsifa tare da cewa nabashi hakuri ko ya saukeni," Yusuf yadanyi jum sannan yace "kina nufin da aka kira inna ba da ke akayi magana ba?" "Ba dani bane, sannan bani kukayi janaiza ba, adiya ce, inna a matsayin mahaifiyarmu naso ace tagane, saidai bataganeba" "Kinata bayaninki angayamiki tasan ku yan biyu ne? Datasan ku yan biyu ne, zata iya tunanin bake bace, anma ke kadai tasani, kuma alokacin sunyi rauni sosai, har tafita kamanninta donhaka bawanda zaiyi tunanin bake bace, kammaninku da duka komai dayane, inma

akwai bawanda zai fahimta acikin halin da aka kawo mana ita” [12/15, 11:17 AM] Benaxir Omar: 1 HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR “Dawannan ma, wanda yadauken a motan nan shine imran, saida yabar anguwan yatabbatar bawanda yabiyomu sannan ya tsaya da motan tareda cewa nafice masa, kuka nahau masa tareda cemasa ko baiwa ne yadaukeni, alokacin tunanina yatike, u wnt understand yazakaji ace yayanka uwa daya uba daya shiyake shirin kasheka, shiya rabaka da danuwanka dakukazo duniya tare, bansan adiya ba, anma nasan zasu kasheta inbani, ta bada rayuwanta don ta ceceni, bayan tasowa datayi cikin rashin galihu da gata, dafarko imran cemin yayi baisan kan gariba, don yazo auren abokinsa ne dasukayi skul daya, kuma ayau zaikoma abj, da ta flight zaibi anma sanin dole a samoni innabi flight yasa yahakura, da motan office dinsu aka kaimu, duk wannan lokacin inbanda kuka babu abinda nakeyi, musamman damukazo fita a radio naji ana sanar da mutuwana, how will u feel, ace da ranka ana sanar da mutuwarka, da ranka bazaka iya shiga gari ba,, harmun hau hanya natuna da wasikar daka bani wanda naki karantawa, atleast i should honour it, hakan yasa nadaga hankalina nace saina koma gydanmu nadauka, kasheni ne kawai imran baiyiba don bakin ciki, acewarsa ni da akace na mutu innaje mezaifaru, dakyar ya lallaboni yace zamuje daredare, nadau risk sosai daredare tabayan window na nashiga, dama akwai yanda nake duruwa nashiga abuna idan nayi jaming kofa, lukily enough baa rufe ba, but dakin arufe take, inajin hayaniyar mutane nashiga na dauko wasikan, da takardun da yayah yabani nayi sighning na kudina, dakuma atms diba, duk wallet dina, potraits din hotunanka harda wasu dan kaya nadiba a karamin jaka najefa ta window

zanfita kenan naji karar key, dasauri na tsaya abayan kofan, mai aikinmu ce tashigo zatadau abu, saidai bata ganeniba, cikin sanya nace mata inkikayi ihu ko kikace kinga mutum saina kasheki, tayi tsit bata motsa ba harna dire natafi” Yusuf yayi murmushi sannan yace “itace tasanar dani taga mutum anma bata gane wayeba, hakan yasa nayi tunnanin kina raye for sure” bata ce komi ba tacigaba da bayaninta ” imran ne yataimakamin mukatafi gidansu, yakuma yi bayani wa umminsa(mahaifiyarsa), takarbeni hannu bibbiyu kuma ta tausayamin, don wlh har karamin hauka nayi, na zauce, ga tsantsan sonka datake cina, gakuma tsantsan tsoron yayah abdullahi dake raina,, wannan dakin dasukaban shima nacikashi da hotunan ka,imran ne yazame min uba, uwa, yaya, kanwa, yataimakamin sosai don baya barina cikin kunci, sannan akowani lokaci idan ina tunanin ku nahau kuka baya iya motsawa saiya tabbatar nayi murmushi, nasan inasonka, anma bansan yazanayiba,saboda zaka fara soyayya dawata idan katuna cewa namutu, ahaka dai ndaure ranan nabude wasikanka nakaranta, wanda saidaya sani nadaman duk abinda nayi tunani akanka wanda karubutamin, nacigaba da rainon soyayyarka, anma imran yana faman dasa nasa soyayyar, banda hanyan kin yarda dashi, bayan gatan dayamin” Wani tsaki yusuf yaja, jin yadda take batunta, tareda cewa “so kina nufin cox imran saved u , nd i didint sai bazaki soyayya daniba, damn it” faruq ne yace “meye haka yusuf, zuciya aitanason me kyautata mata, kaida kake da ikon kareta ba kin furta mata soyayyan kayiba, am quite sure daka fadamata shell atleast have trust on u” hannu yusuf yasawa faruq alamun yayi shiru tareda janyo amira cikin fushi, idonta ya gwalalo tazaroshi yace “u beta choose kafin na wurgaki a tsakiyan titin nan, ni ko

imran!
[12/16, 9:31 AM] Benaxir Omar:2️⃣HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Zura masa ido tayi, dataga tabbas dagaske yake zai iya cillata a tunaninta, tafara dan kara don damkar dayayi mata, hakan yasa yasaketa, bai kulataba yacewa faruq sutafi, Cikin gari suka koma, suka kaita gun motarta, sannan yace tacigaba da zama zaikoma bauchi, zaikuma saka abdullahi a kotu, taji tsoro don har gwalalo ido tayi, tareda cewa “karufamin asiri, koba komi danuwanane, zanhakura nabiku kawai, saidai dole kudau mataki akanshi, banda zuwa kotu,tamkar tona asirin gydanmu ne,” ya yarda dahakan, anma yace mata “kindai san hukuncin kisa ko, kashe yaruwarki yayi akan dukiya,donhaka dole amasa hukuncin data dace dashi” zatayi magana yasa hannu yarufe bakin, hakan yasa tayi shiru, tana zaune a motan, yakura mata ido, babu abunda baya kissawa ransa, godiya yakewa Allah daya taimakeshi yakuma ceceshi yanuna masa baiwar Allshn nan, juyawa yayi yatafi bayan yadau numban wayanta,zama tayi dakyau takalli steyerin motan, tana buga kirjinta tareda cewa “weldone amiraa, kinyi kokari, Allah ya dada kareki, kinyi kokari dakika danne son dakike masa, dakika danne shaidan kika nemi kariya daga Allah” itakanta tasan cewa yadda tadade bata ganshi ba, Allah kadai yasan yadda takeji, kuma tayi mamakin yadda akayi yusuf yakoyi magana, mutumin da magana ke sasa ciwon kai, uhmm kowacce gauta ja ne, kunna motar tayi tanufi gyda, tana shigowa falon taga imran, dogo ne iya dogon namiji donkuwa yafi yusuf tsayi, zubinsa na larabawa tunda kansa bakin gashine akwance, gashi namiji mai son ado bayan yasan halittar kyaun da Allah yamasa, idonsa manya manya saidai sunanan ne very sexy, saboda yana abu kaman mai jin bacci,

ayadda yataso tasan mezaice dasauri tace “i went to visit a frnd” yadan dakata sannan yace “But you should have called nd explained, ” bata ce komi ba tazauna akan lausassan kujeran tana lumshe ido, tunaninta shine yusuf, shikuwa imran kallon daya mata jikinsa yabasa akwai damuwa, arayuwa babu abunda ya tsana irin yaganta awani hali, yazauna gefe bata saniba, yamiko hannunsa yadafa jikinta zaiyi magana, dasauri tabude ido tareda cewa “i have told u tymz without number, kadena tabani!, ni ba muharramarka bace, haramunne i repeat HARAMUN ne katabani ko dakuwa yayane” “Am sorry i jex cnt control my emotions ne” ” den saika ambaci Allah, shaidan ne yake rudarka, kuma i have to leave dix house, saboda kullum inafada maka baka yadda, kar wataran ummi tafita ni dakai kamin ba daidai ba, ” “Nooo wlh nadena, don Allah nadena wlh, i wnt come near u” “Beta” [12/16, 9:50 AM] Benaxir Omar: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Don ita tasani shigan kare mutuncinta tanayi don karta shiga hakkinsa, saidai talura yafiye son jiki ne, namiji ne mai son mace, donhakane take daure masa bata masa wasa, Shiru yayi sannan yaja gefe, hannunsa akansa, tahaura sama dontayi wanka tacanja Washegari dassasafe yusuf suka kama hanyan bauchi, suna isowa, wanka yayi ya sallah,sannan yanufi gydansu ramlat,tanna zaune tana jiranshi da tarin takardu agabanta, idonta a kumbure, donkuwa yau mahaifiyarta ta tukota, lalle lalle tafidda miji, kokuwa dangin ubanta su aura mata wani, tarasa yazatayi, taci kukanta takoshi Yana zama yalura da yanayinta donhaka yace “meya faru?” “Babu komi” “Sure?” “Positive” Hakan yasa yaci gaba da duba takardun, lalle ramlat tacika aikinta, takuma bashi mamaki, domin kuwa, hatta asibitin da aka haifi su adiya da amira saidata nemo, ga sunan gakuma certificate

of birth, ta bibiyi gidan marayu, takarbo duk wasu bayanai tun randa aka kai adiya, har randa aka karbota, in d name of mutum daya, abdullahi amir, baiyi mamaki sosai ba, sunsaba ganin wannan case din, yan ciki daya su kashe juna saboda dukiya, dayakashe mahaifinsa saboda kudi. Yaduba hotunan scene din, wanda ita ramlat takarbo alokacin mutuwan adiya, saikuma hoton adiya dakuma hoton amira, yasa agabansa yana kallo, babu banbanci illa amira tafi adiya haske, yanayinta na hutu yafi bayyana, saikuma adiya tanada tawadan Allah dankarami agefen kumatunta wanda yakara tabbatar masa da ae lallai, inhar bawanda yasan akwai yan biyu ba babu wanda zaiyi tsammani cewa ba amira bace, banbancinsu kadan ne, ya ajiye sannan yadau file din dukiyan, yakalli makudan kudin, lalle kudin yayi yawa da abdullahi ko ya mallakesu aganinsa bazai taba talauci ba inba ikon Allah ba, nan yaji tausayin inna, gashi baiwar Allah harda aiki takeyi, kanshi a kasa yaga abu yadiga akan takardan, yadago kansa dan dubawa yaga menene ga mamakinsa, saiyaga hawaye ne fam a fiskanta, ramlat ba gwanar kuka bace, kozatayi bazatayi agabansa hakan yatabbatar masa da alamarin yasha kanta ne, ya ajiye littafin tareda cewa “Can you share the story?” Bata amsa ba takara fashewa dawani kukan kaman yasanar da ita mutuwar iyayenta, shiru yayi yana kokarin karantarta don yaga meye matsalan, anma yagagara ganewa, ayadda take kukan kawai ya zaro handkerchief yamika mata tana gogewa, yazura mata ido harta gama kukan, sannan yace “You can talk” Bata amsa ba sai bayan mintuna, sannan tace “Ka min alkawari zakamin wani abu donAllah” “Inzan iya zan yi” “Zaka iya, abu mai sauki ne don Allah” “Toh nayi, menene?” ” ka aureni”
[12/16, 9:50 AM] Indo: HANNU DAYA

BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR
Don ita tasani shigan kare mutuncinta tanayi don karta shiga hakkinsa, saidai talura yafiye son jiki ne, namiji ne mai son mace, donhakane take daure masa bata masa wasa, Shiru yayi sannan yaja gefe, hannunsa akansa, tahaura sama dontayi wanka tacanja Washegari dassasafe yusuf suka kama hanyan bauchi, suna isowa, wanka yayi ya sallah,sannan yanufi gydansu ramlat,tanna zaune tana jiranshi da tarin takardu agabanta, idonta a kumbure, donkuwa yau mahaifiyarta ta tukota, lalle lalle tafidda miji, kokuwa dangin ubanta su aura mata wani, tarasa yazatayi, taci kukanta takoshi Yana zama yalura da yanayinta donhaka yace “meya faru?” “Babu komi” “Sure?” “Positive” Hakan yasa yaci gaba da duba takardun, lalle ramlat tacika aikinta, takuma bashi mamaki, domin kuwa, hatta asibitin da aka haifi su adiya da amira saidata nemo, ga sunan gakuma certificate of birth, ta bibiyi gidan marayu, takarbo duk wasu bayanai tun randa aka kai adiya, har randa aka karbota, in d name of mutum daya, abdullahi amir, baiyi mamaki sosai ba, sunsaba ganin wannan case din, yan ciki daya su kashe juna saboda dukiya, dayakashe mahaifinsa saboda kudi. Yaduba hotunan scene din, wanda ita ramlat takarbo alokacin mutuwan adiya, saikuma hoton adiya dakuma hoton amira, yasa agabansa yana kallo, babu banbanci illa amira tafi adiya haske, yanayinta na hutu yafi bayyana, saikuma adiya tanada tawadan Allah dankarami agefen kumatunta wanda yakara tabbatar masa da ae lallai, inhar bawanda yasan akwai yan biyu ba babu wanda zaiyi tsammani cewa ba amira bace, banbancinsu kadan ne, ya ajiye sannan yadau file din dukiyan, yakalli makudan kudin, lalle kudin yayi yawa da abdullahi ko ya mallakesu aganinsa bazai taba talauci ba inba ikon

Allah ba, nan yaji tausayin inna, gashi baiwar Allah harda aiki takeyi, kanshi a kasa yaga abu yadiga akan takardan, yadago kansa dan dubawa yaga menene ga mamakinsa, saiyaga hawaye ne fam a fiskanta, ramlat ba gwanar kuka bace, kozatayi bazatayi agabansa hakan yatabbatar masa da alamarin yasha kanta ne, ya ajiye littafin tareda cewa “Can you share the story?” Bata amsa ba takara fashewa dawani kukan kaman yasanar da ita mutuwar iyayenta, shiru yayi yana kokarin karantarta don yaga meye matsalan, anma yagagara ganewa, ayadda take kukan kawai ya zaro handkerchief yamika mata tana gogewa, yazura mata ido harta gama kukan, sannan yace “You can talk” Bata amsa ba sai bayan mintuna, sannan tace “Ka min alkawari zakamin wani abu donAllah” “Inzan iya zan yi” “Zaka iya, abu mai sauki ne don Allah” “Toh nayi, menene?” ” ka aureni” [12/19, 7:52 PM] Indo: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Shiru yayi, shi bai fahimci mai takeso daya ba, yasan ko sama da kasa zata hade auren ramlat ba nashi bane, ko kishin amira wani tashin hankali ne, balle shikanshi yasan cewa bazai iya zama da ita ba, sanadin ruhinsa na gun amira, saidai ta auri gangar jikinsa, yaja numfashi sannan yace “kiban lokaci muyi magana” Ta share kwallan daya fito mata sannan tace “babu wani dadewa sati daya akaban agyda” Wani nauyi yaji zuciyarsa yayi sannan yace “naji ill get bck to u” Tashi yayi yafice, batada abokin shawara, shiru tayi, don numfashinta daukewa yakeyi yana dawowa, kaman andanna mata abu a zuciya, tayi shiru tana tunani Shikuwa yusuf yana fitowa, dayaja motarsa yanufi office, yazauna tunanin maganan da ramlat tamasa yakeyi, auren ramlat barazanane agareshi, inya aureta riba biyu zaisamu, zata taimaka wajen kawar da

abdullahi, sannan a saninshi da ita, macece mai kamun kai, inkuwa yaki zata iya resighning a case din, kuma zata iya rabuwa da alamarinshi don aure zaa mata, waya yadauka sannan yakira amira, “Hello yakike?” “Lafiya kalao ya gari” “Kalao, hope komi lafiya?” “Ae, alhmdlh, ” “Inada magana” Tayi tsit sannan tace “Mekenan?” “Maganan case dinmu, da lawyern” “Awhh kana nufin ramlat?” “Ae, aina kika santa?” “Uhm, ka amince da auren nata?” Dum!, ya akayi tasan komi, (Don Allah kumin afuwa kunjini shiru,ciwo ne ya kwantar dani har gadon asibiti, a kwantar atayar, Allah dai yabamu lafiya, wanda suka sani suke kirana nagode muku Allah bar zumunci)
[12/24, 7:03 AM] Benaxir Omar: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Shiru yayi don mamakin metake cewa, baitaba zaton cewa tasani ba donhaka saiyace “shine nazo neman shawara” “In nine ka amince, aidole ita zata taimaka mana” “Kidai sake tunani” “Tunanin kenan” Baibata amsaba canja tadin yayi har ya kashe wayan, Shidai jikinsa na basa ba don Allah amira ta aminceba,yadaiyi shiru yana tunanin mezaiyi wanda bazaiyi nadama ba, Amira kuwa tana kwance ne ummi tashigo tamata sallama akan zataje gun aiki, tafito ta rakata tana murmushi, dawowanta kawai tamike takkwanta akan kujera bacci ya kwasheta, jitayi ana shafata, kasancewarta mai son jiki saita kara langwamewa azatonta mafarki take, saikawai taji shafen yana karuwa don haka , bude idonta tayi aikuwa taga imran akanta, salati tayi tamike tareda cewa “meye haka?” “Don Allah kiyi hakuri karki gujeni,” “I told u kadena tabani, meye hakan? Ni ba muharammarka bane, bawai ina kyamarka bane, Allah ne yayi hani dahakan, kai balarabe kamata yayi kasan wannan kake taka sani, kabari in Allah yayi ni matarka ce, zaka tabani yadda kakeso,

yayi shiru don shi acikin matan daya hadu dasu, bakomi bane idan yataba yanmata, ko ya rungumesu, yana ganin kaman duk acikin wayewa ne, hakama yanmatan ko baya tabasu dakansu zasu fara rikoshi, anma amira daban ce hakan yakaro martaba da girmanta a fuskansa [12/24, 7:39 AM] Benaxir Omar: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Ramlat ne da yusuf tareda farzan wanda suke zaune da alkali a chamber suna zaune inda ramlat take bada hakuri takuma janye karan da suka shigar, farzan cikin bacin rai yamike yace, “wannan ma ai bayi bane, weve wasted our time, we r being accused, kujanye mu mushigar, bamu yarda ba, client dina tasha wahala, for Godsake almost two months,” Alkali ne yadaga mai hannu kafin yanemi afuwa yazauna, nan alkalin yace meyakeso ayi tunda basu hakura ba “Defamation of character, donhaka zamu shigar da kara kotu,” dawannan suka rabu, aranan aka fitar da nads, tayi baki ta kode, ta dawo abun tausayi,, suka fito yusuf na tsaye kanshi a kasa, yagagara hada ido da ita, suka shiga mota suka wuce, yusuf office dinsa yanufa, yana zaune abdullahi yashiga hankali atashe, yana cewa “naji kunjanye kara, meya faru? Zakabar azzzalumar yarinyannan tabar hannunmu” Yusuf yayi murmushi sannan yace “bakomi fa, naga babu cigaba ne a alamarin, shiyasa na hakura, ” “Anmadai yusuf kasan yakamata tafuskanci hukunci ko” “Ae zamuyi shawara daga baya, ni na kai karan kuma ni na janye” Hakan yasa abdullahi fita a fusace, yusuf yayi murmushi don dai mamaki kam bai barshiba Nads na shigowa gyda daki tanufa, tashiga bandaki wanka tayi donkuwa tafi awa uku a bandaki don cire kazantar jikinta, tana fitowa daddynta na falo tahau table din tazauna sannan tace “daddy yanaga ranka abace kaida zakayi murna?” “Wani murna nadiya?,

anbatamiki image, sharrin kissa of all tinx aidole raina yabaci, dole mushigar da kara kotu" [12/24, 7:54 AM] Benaxir Omar: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR "No daddy, nikam nahakura wlh, kurabu dasu ko tararsu kar aci" "You r out of ur sense, haryanzu bazaki daina sonshi ba ko? Bakida zuciya ne?" "Daddy wlh nagagara ganin laifinsa, ina sonsa ahaka, kataimaka don haka kahakura karku shigar da kara" Baikulataba yafice, kasancewar ya saba da yar tasa dole yabarta, naci da kafiya acikinta, ci tayi sosai kaman ba itaba, saidai tanagama ci tabarke da amai, aikuwa nan akayi da ita asibiti, zazzabi ne mai zafi da typhoid yarufeta, mummy dai hadiye raine batayi tamutu ba don bakin ciki, itadai damuwarta ashigar da kara kotu,, Abdullahi hankalinsa yatashi, jikinsa nabasa ba lafiya ba, don ko daya tunkari inna da maganar cewa tayi sudau dangana, Dasafe yusuf yakira amira tabiyo flight, don yanaso aranan yagabatar da ita gun inna donma yasanar da ita yana zuwa, abdullahi kuwa jinhaka yasa yaki fita yana makale, yusuf dakanshi yadau amira a airpot yakaita gyda, suna shiga falon inna taganta, mikewa tayi a razane zata gudu don azatonta fatalwa tagani, abdullahi kuwa da ace faduwar gaba nasa mutuwa daya hadiyi ransa yamutu ********alokacin da suke can suke rikicin kallo kallo, feena wacce tazobin junction taga yusif da amira tuni ta isa asibiti don dama zatazo mata murnan fitowa, kawai taga yusuf da amira abun yabata mamaki. Dondai tasan amira batada wata yaruwa dazata lakama da ita, tana isa asibitin suka gaysa da amira wacce take shan drip tayi murmushi suka gaysa sannan tace "nikuwa amira nada wata yaruwa ne?" "Mekika gani?" "Naga exactly ita, da yusuf yanzu a traffic" Gabanta yayi mummunan faduwa

12/28, 7:02 PM] Adda Bena: HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINNKA NA BENAXIR OMAR tayi kasaf tana kallonta,"babu wani amira dakike gani ke duk abinda zaidaga min hankali naga sonshi kikeyi, " "kai nads, wlh tlh dagaske nake,gwada kiransa ko zai dauka!" mika mata wayan tayi takarba tayi dialling numban Yusuf dama number nakanta ta haddace, ***** Inna tayi jigim alokacin da Yusuf take cewa inna yarki CE, ta cikinki, amira CE, amira dagudu tanufi mahaifiyarta wasu zafafan hawaye ne suka zubowa inna yayinda tariko amira, tabbas amira ce, sunfi mintuna ahaka abdullahi na tsaye kaman zai gudu idonshi ta fiffito, kawai saiyarike kai yafara kurma ihu hakan yajawo hankalinsu gaba daya kanshi, yafara cire kayan jikinsa dasauri Yusuf yanufeshi zaicire masa anma baisamu dama ba, alokacin wayansa take kara dubawan dazaiyi yaga bakon numba, yana dauka yaji nads tace hello, dasauri yakashe, yakoma kan abdullahi, fadefade yafarayi, abun mamaki yana cewa "dama Dan iro yace ana ganinta zanyi hauka, tsafin baiyiba, nakashe yaruwarta ma adiya, Wanda kika Haifa a asibiti nakaita gydan marayu tareda hadin bakin nurse, amiran ma naso dauketa muce tarasu mubaki wata, Allah ne yasa kika farka dawuri, dukiyan baba nakesonci dukka nikadai, banso muraba dawasu" yana gama fada yafita da gudu alokacon Yusuf yabishi tareda cewa masu aiki su kamashi, yanken jiki inna tayi tafadi amira tasaka wani kukan, wayanta tadauko takira numban nanatu, wacce ganin numban dabatasaniba tadauka tayi shiru, amira race "nanantu , muhadu a asibiti, inna balafiya" tana fada takashe, itadai nanatu tasan muryan amira taji, toh ko watace daban, donhaka tamike tasa hijabi tatari kekenapep, yayinda Yusuf yayi gidan mahaukata da abdullahi asalin hauka yayi, [12/28, 7:18 PM] Adda Bena: HANNU DAYA BAYA

DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Suna isa asibitin akabata gado, sunasamu tafarfado alokacin hawaye sai match past sukeyi a idon amira, nanatu tashigo,ganin amira yasa ta yarda purse dinta ta falla da gudu saida amira tayi dariya tsabar mamaki, can dai takara Kiran nanatu tareda cemata tazo itace, tukun nanatu tazo duk dahaka tana nesa nesa da ita, bakin ciki daya gulli amira yasa ta duma mata dundu tareda cewa “fatalwa baya dukan mutum, sau nawa zancemiki nine?,” hawaye suka biyo idon nanatu tarungumeta, tana kuka, hakan yasa amira ma kuka, farkawar inna CE tadawo dasu hankalinsu, inna na zubar da hawaye tana magana “duk kokarina na yin adalci a tsakaninku nayi, amma abdullahi baici gadon sunansa ba, wannan halin dayayi bana bayin Allah bane, wacce irin son abun duniya CE zatasaka ka illata yanuwanka na jini, kaiconka abdullahi bazammaka baki ba, Allah yamaka albarka kuma ya shiryeka, anma tabbas hakkin adiya sai Allah Yakama ka dashi , bazanmaka baki Allah yakara tsanwantar maka da fushinsa ba, kaiconka abdullahi,” Amirace tafara bawa inna hakuri kafin tayi shiru, duk da nanatu batasan kan maganan ba, anma tagane me ya dosa, Yusuf bayan kaishi asibitin mahaukata baibar gunba saida yatabbatar antsayar da likita, sunyi dube dubensu sunce ba abunda yasameshi, yadai bar asibitin akan zaidawo kafin yawuce asibitn da inna take, tana ganimshi tacigaba da masa addua, tanasa mishi albarka harsu kazrat sukazo, asibitn yadan cika don maman sadiq ma tazo duo dataji wannan mummunan labarin baimata dadiba, daredare suka watse aka bar amira takwana, duk da tana ganin Koran imran taki dauka * koda nads takira yaki dauka bari tayi damuwanta a sallameta, zaiga yadda ake naci duk dacewa takoyi darasi babba na iyawa da bakinta, kiyayye harshe Kasan

lafazinka ka tauna kafin ka furta, sannan harshe guba ita takesa mutum acikin wani hali. washegari aka sallami inna, babu yadda Yusuf baiyi taje taga abdullahi ba taki, hakan yasa yabarta, taje gyda nanda kofa bata bari amira taje , labari kuwa yazama hot cake yabaza garin bauchi dagefen nahiyar, nacewa yaya uwa daya uba daya yakashe kawarsa daya, Allah baibashi saan dayan ba, yahaukace, labarin mutuwan amira kuwa shima yabazu cewa bata mutuba, kai da kwarkwata agarin bauchi sunsam da maganan, [12/28, 7:23 PM] Adda Bena HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Yusuf na iya kokarinsa ganin abdullahi ya sami lafiya Anma Abu yaci tura, inna ta tsaida maganan cewa amira takarbi companyn tunda itace tayi saura, hankalinta yafara kwanciya bayam tagayawa inna Wanda suka taimaka mata, inna tace su shirya suje don sumika godiyarsu dakuma nuna farincikinsu, yayinda yusuf yashiga mawuyacin hali na yanmata Zara Zara dasuke gabanshi tundaga kan AMIRA, NADS, ,RAMLAT, masu karatu wazai aura wazai bari?, biiznillah gobe zangama littafi insha Allah duk yawanshi, sannan ya batun imran? wazaa basa a yanmatan??sannan ya future din farzan??
i dont. knw which words to use to thank my blog members, fella nagode nagodee, miyyettti,shukran kathir, thank you soo much, wlh tears roll down as i saw how you all wished me well, nagode Allah yabar zumunci, yabar kauna, as of dix dat request my num, m sorry but for security purpose m afraid, u can search my facebook account benaxir omar nd we shall talk, nagode nagodee jiki nawarke alhamdlh
[12/30, 5:06 PM] Benaxir Omar:1️⃣HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Ran jummaa suka shiga garin abj, yusuf ne mai jansu, amira agefe inna da

kazrat abaya, suna isa dama amira tagayawa imran dazuwansu, sunshiryawa zuwan nasu, tabbas sunga karamci, inna taji dadi aranta takuma yaba da halin su, da ace babu yusuf, da zata bawa amira imran saidai gwagwarmayan da ya musu ko ita takawo butulci duniya bazata hanashi auren amira ba, inna tayi godiya sosai, sunje musu da goma ta arziki duk da sunsan su imran dinma akwai arziki, imran ganin yusuf kadai saida ya sanya masa zuciya, gwiwarsa tayi sanyi musamman lokacin da inna take bada tarihin amira, yaji duk son dayake mata baikamo yadda yusuf yake mata, duk da shima yataka rawar gani anma yasan ko zai nace zaishiga rayuwansu ko sune bazaiji dadin amasa haka ba, donhaka ya sosa keya yana kallon kazrat tareda cewa yusuf "kozamu saka labule ne,?" Yusif yagane don haka murmushi yayi baice komi ba yayinda itakuma kazrat kunya kaman yakasheta, itama taji yaburgeta alokacin, agurguje suka shirya zasu fice donkar dare yamusu akan hanya, saida imran yatabbatar yakarbi numban kazrat agun amira suka tafi, tun ahanya yakafa kiranta harsuka isa, inna dai farinciki ya isheta koba komi anrabu Ify [12/30, 5:17 PM] Benaxir Omar:2️⃣HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Suna isowa bauchi saida yasaukesu a gyda kafin yakoma gyda, kazrat kam zuwanta abj yafi zuwan gov., Washegari dasafe saturday karfe 3 yusuf yakira ta tana zaune ta sha kwaliyya tayi kyau, yace tashirya yanaso tarakasa wani gu, tadanyi jum don tasan inna sarai, ita bata fiyeson fice fice dinnan ba, mace mai mutunci da kamala dakuma kamun kai ba girmanta bane ko mutunci saurayi yadauketa suyita yawo ko wani abu, duk da kusancinsu da yusuf din ko data gayawa inna saidata sha tambayoyi kafin innar tabarta, bayan laasar yazo, abaya ne baki ajikinta tashiga motan tazauna

kamshin turaren jikinta da nasa ne yacika motar, yaja numfashi yana lumshewa, tadan tsume fuska sannan tace “meye” “Babu, kamshin jikinki daban ne, kominki daban ne, Allah barmu tare” Bata bashi amsa ba, don haryau atunaninta bai fara datn dinta ba, sai hanya dayakebi, [12/30, 5:56 PM] Benaxir Omar: 3 HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Hanyan insurance house yanufa da ita, suka shiga wani gu daily meals, takaranta aranta sannan tayi ajiyar rai, bude mata motan yayi sannan tafito suka jera, sunyi kyau sosai domin shadda ce fara sol gezner ajikinsa, tafito da kyaunsa. Hanyan shiga sukayi suna budewa kafin tashiga yabata kyalle yace kirufe fuskanki, haka yasa tarufe Fuska data shiga ji tayi ana “happy bday to you!!!” Kafin yacire mata kyauren fuskan nata, wani murmushi tayi don ganin mutanen, nanatu, mamancy, maryam maleka, dayyiba, kazrat,ramlat, har wadanda bata saniba, sai da kwalla yafitomata, tsabar ganin yanuwa da abokan arziki,taji dadi sai alokacin tatuna cewa yau ne bday dinta, yusuf ya matso gabanta sannan yace “monkey!!, u dnt even knw its ur bday” Ta turo baki tareda cewa “ni ne monkeyn?,thnk” Dariya yayi wanda yafitar da kyaunsa, sunci sunkoshi, abun yayina masu kamun kaiba kida ba komi, saiwani katon cake datagani, cake din yahadu iya haduwa, nan akaje tayanka cake, dandanawa dazatayi taji wani dadihar bakinta saida tajuyo tace wa yusuf “wayayi wannan cake din?” “Santi kikeyine?” “Noo, wlh yayi dadi ne” “Oho nima reference akaban, kitambayi kawarki nanatu” Nan dai suka bata gifts, anan yusuf yayi gyran murya sannan yace “on this medium, ill like to confess something,” donhaka dukka saisukayi concentrating kowa na sauraronsa sunason jin mezaice “Imet this lady 3yrs back, since from den. She has been my heart,soul,nd

heart, i yusuf yarima bauchi declare that i love her and ill marry her!, she owns my hrt alone, nd no woman has my her except her," wani tafi aketayi, amira kaman tayi kuka, hawaye na bin idonta harta isa gun, ji yayi kaman ya rungumota, nan yayi auzubillah acikin ransa, tana zuwa ta tsaya cak, ya tsugunna yaciro wani zobe a aljihunsa sannan ya miko hannunsa, kyallin zoben ya ishesu diamond ce fal, tamiko yatsanta yasaka mata, hannunta abaki tana kokarin rufe farin cikinta, hawaye ya cika mata fuska, batasan mezatace ba [12/30, 6:20 PM] Benaxir Omar: 4 HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Tabbas yau yazame mata ranar farin ciki, ranar da bazata taba mantawa ba, yusuf yashare mata bakin cikinta ba, baitaba furta mata kalmomin dasuka mata dadi irn na ranar ba, tuni aka fara watsewa bayan jawabin godiya datayi, saida kowa ya watse sannan suka dawo, ana kiran magrib , inna sai ganinta tayi da gifts a zube, nan amira tagayamata tana farinciki, "inna yau yusuf yafadamin," inna tayita murmushi itama murna take yartata tana cikin kwanciyan hankali, daki amira taje takunna kida tasha rawan shoki, sekem da shakiti bobo, har numfashinta yafara daukewa kafin tashiga tayi wanka tafito takwanta sai bacci dama bata sallah *** Tunda aka kirata aka sanar da ita yusif yahada gagarunar bday wa amira hankalinta yatashi tas ya tsaya, gashi bata isa tace zataje ba, tayita kiran wayan yusuf yaki dauka,, ko mummy saidata mata magana amma nads kuka tafarayi, musamman da aka turo mata hoton yusuf lokacin dayake sanyawa amira zobe a hannu, iphone din hannunta tazubar akasa, saida yayi kara, kuka tafarayi tsakanimta da Allah ganin ba hanya mummy tarufo kofan tarufeta, ranan bacci bai isheta ba, saida mummy takara lekowa tazaunar da ita sannan tace, "nadiya

rayuwa dakike gani babu tsanani babu wahala, shekaranki nawa kina haukan son bawan Allahn nan, kiga wahalan dakika sha , ko kece autar mata ai albarka, Allah yace ki rokeshi zai amsa miki, ina mamakin yanmatan dazaku ta wahala akan namiji, soyayya tayita baku wahala, inkigaka kina son mutum abu baya tafiya daidai infact ko daidai yake tafiya, dage da istihara, wlh babu wacce zata gina rayuwanta akan istihara ta wulakanta, babu!, kiga yadda rayuwarki ta dawo, haba nadiya, duk abinda zakiyi kinemi shawaran Allah zakici riba, kinafara ostihara inba alheri bane yanzu zakiji yafita akanki, ke kanki wani nutsuwa zakiji, ko bata miki rai abu keyi, shimfida sallaya kikai kara gun Allah, bazaki taba tabewa, rayuwarki tazama akan istikhara, baizama dole sai maza biyu ba, hatta abu zakiyi kinemi zabin Allah, makaranta etc, Allah zabamin alheri, ko ka musanya min, yanzu yanzu Allah zai magancemiki" Nads tana kuka har aka gama mata waazi, mummy nafita tafita tadauro alwalanta, tafara sallah, tafara kai kukanta gun Allah in alheri ne Allah yabata in sharri ne Allah yaraba, m so soorryy bancika alkawari ba, amin afuwa, but nxt insha Allah [1/1, 7:59 PM] Benaxir Omar: 65HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Amira washegari bacci mai dadi tayi tadade bata ji wannan kwanciyan hankalin ba, alokacin kuwa yusuf tuni yayi magana da waliyyinsa za azo nema masa auren amira, jira yake ta tashi ya sanar da ita, ko da ta tashi ta fito falo sanye da rigan bacci sai ganin shi kawai tayi, dagudu takoma tasako hijabi tana ta mita meyasa ba'a fada mata ba, sai alokacin talura inna bata nan tafita aiki, don haka tafito duk kunyar shi ta isheta, ya ce "Alfarma nake nema a bani daman turowa" Ta yi kif da ido sannan ta ce "ni ma ina da tawa alfarman" Kunnensa yarike alamun yanajinta "Ina so idan anyi

tambayar, ahada aje ayi na gidan su ramlat” Shiru yayi mamaki ta ishe shi, in ba mace mai karfin hali ba, ba kowacce mace zata jure ayi auren ta da wata daban ba, godiya yayi mata sosai A ran ta kuwa cewa tayi “A man is always a man” duk wani cewa da yakeyi ba ya son ramlat yana wani rawan kai akan ta, ba musu ya amince, itadai damuwan ta as far as itace major shareholder ai magana tazo dasauki, Acikin kwana uku aka yi tambayan Ramlat da Amira, wacce ita ramlat batasan anyiba, dawowan ta daga office kawai sai taga mahaifiyar ta na farin ciki, abun ya isheta can ta daure ta ce 66HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR “Ni kuwa meya faru yau?, naga sai murna kike?” “Aww tambayata kike? Dakika turo mijin aure ai magana dole nayi farin ciki, mu ne da godiya tunda Allah ya karkado hankalinsa kanki” Ramlat tayi jum tana tunani, tasan idan takara tambaya daya ko biyu inna zata ce ta raina mata hankali ne, don haka ta wuce daki kawai, mai aikin da tazo wanke mata toilet ta tambaya nan ta sanar da ita ai daga gidansu Yusuf ne sukazo tambayan aurenta, bata yarda ba sai da tarinka rantse mata, tadauko wayan ta sai alokacin taga text din shi “I’ve finally decide to choose two wives, i hope u’ll colaborate” Ajiye wayan tayi, tace mai aikin tafito tashiga tayi alwala, tazo tazuba sujjada, tayi rakaa biyu ta godewa Allah harda hawayenta, domin kuwa shine buwayi, shine mai jinkai, tabbas ta yarda duk wanda yakoma ga Allah bazai tabeba, tadage da istikarah, da addua’n alheri sai gashi Allah yanuna mata, tuni tafara kiran close friends dinta tana sanar dasu, Nads tayi sati guda tana addu’oi cikin ikon Allah abunda bata taba mafarki ba shi ya faru, wato ji tayi son Yusuf yafice aranta kamar yadda ake cire tsumma a randa, taji kwata kwata bata muradinsa sai son Farzan

kuma data ji ya kwanta mata a rai, nan ta sanar da mammy , mammy ta tambayeta ko farzan din na neman ta? Ta nuna mata txt dayake tura mata da kuma yawan kiran ta dayake yi bata dauka [1/1, 8:15 PM] Benaxir Omar: 67HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Mammy ta ce “ki ci gaba da adduo'in ki, in alheri ne Allah ya tabbatar, ko da taji labarin yusuf ya kai tambayan gidansu Ramlat da Amira anan ta rinka mamaki, lalle Allah ya ceceta domin kuwa da har lokacin tana son shi, zata iya hadiye rai ta mutu, ko ba komi son da take mishi yakoya mata darasi daya zuwa biyu, mutum ya iya bakin sa, kowani kalma zai iya zama alheri ko sharri donhaka ne yafi dacewa mu tauna lafuzanmu kafin mu furta, na biyu duk wanda zaiyi soyayya wanda bazai koma ga Allah ba yana cikin hallaka, gashi yanzu ta amince wa farzan dinta, yana sonta fiye da tunaninta tabbas ka So a So ka shine So. Daga gydan su yusuf aka roki alfarman asaka ranar auren tunda mata biyu zai aure kuma aka amince masa, nan aka hada dana Kazrat wanda itama imran ya matsu ayi aure, Rana daya akasa auren Kazrat da Imran Ramlat da Amira wa jarumi Yusuf domin kuwa jarumi ne zai auri mata biyu a lokaci daya, kowanne fanni suna shirye shirye ba kama hannun yaro, alokacin yusuf yayi iya kokarinsa don ganin yaciro abdullah iatleast yaga auren kanwar sa, anma suka bashi shawara wanan ciwon sai warakan Allah, donhaka ne yasaka malamai aka tafi dashi don mishi magani Wata daya akasa bikin, alokacin Nads ta tura sakon congrats wa amira cikin farin ciki amira ta maida mata, harda zuwa kai mata katin biki, anan Nads tanuna mata Farzan amira ta mata murna don Nads tace suma wata biyu akasa shirye shiryen suke, Amira tayi mamaki sosai ganin yadda nads ta nutsu ta dawo mutum, mace mai hankali. Su nanatu ,

maryam, mamancy, da dayyiba yan rawan kai sune manyan kawayen amarya kuma sun gwangwaje suma sunanan suna jira, don nima benaxir ashobe nayi abuna, zamuje mu gwangwaje muyi shakiti bobo.68HANNU BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Ran Asabar aka daura Auren Amira kafin na Ramlat a matsayinsu na matan Yusuf, yayinda Kazrat kuma da Imran sunga larabawa kam ba laifi. Gida babba ya gina musu a g.r.a kowacce da fannninta 3 bedroom each, babu wacce zatasan me ake ciki, kuma kowacce yabata mukullin mota, dadin sa daya dukka su sunada ilmi, wayewa da kuma hankali, donhaka kishin su bazai basa matsala ba, Dakin Amira aka fara tarewa kafin na Ramlat, (nidai tunda muka kawo amarya aka bamu kudin sallamar mu shikenan muka watse, details kuma Allah yabar wa kansa sani). Nads tanata shirin nata itama, wanda Farzan yafi ta gandoki, sunfara event (shima ana kawo ashobe na dauka namika wa tela na yamin dinki, don muje musha rawa). Tabbas biki yayi kyau, (mun ci mun goge wuya munkuma yi rawa), biki ne na yayan manya shima, itakuma gidanta na gida dubu aka kaita aka watse, [1/1, 8:28 PM] Benaxir Omar:69HANNU DAYA BAYA DAUKAN JINKA NA BENAXIR OMAR Dama Kazrat abuja aka wuce da ita, donhaka masu zuwa sukaje Abdullahi baisamu lafiya ba sai kusan wata biyu, dakyar aka cire asirin jikin sa, a lokacin yusuf ne kadai yaje malamin ya masa bayanin cewa asiri ne sosai akayi , mai kuma karfi wanda daya karye yakoma kansa. Abdullahi yadawo abun tausayi Yusuf ne yadaukoshi a mota suka dawo , Amira tasa masa ruwan wanka yayi, duk tanayi tana hawaye shima hawayen yake cike da nadaman abunda ya aikata, bayan yayi wankan suka shirya gaba daya don zuwa su roki inna ko zata yafe mai, Inna kin kallonsu

tayi, saida Amira ta sha kuka, shima Abdullahin kuka yayi tayi yana rike kafafunta yana rokonta gafara dakyar ta amince da sharadin zai biya diya, yakuma yi azumi, ya amince anan yafara samun nutsuwa, Amira suka tafi suka barshi. Zaman lafiya suna kokarin yi daga Amira har Ramlat suna bada hakkin zaman aure kowacce tana kishin ta cikin aji da wayewa, shi kadai zai iya gane hakan. Lalle mata biyu rahama ne, domin shi kam yayi dace, Allah yakara hada kan su ya kori shaidan , lokaci daya suka sami ciki, (abun ba acewa komi sai godiyan Allah). Ni dai Benaxir danaga nagama ganin labarin nake cewa BISALLAM, Anan na kawo karshen labarin , dafatan mundauki darussan dake ciki, Ubangiji Allah yasa mu gyra, Na sadaukar da Wannan littafin zuwa ga Hanifa usman Maryam maleka Maman ahmad lagos Hauwa mudi Ummi Aisha Luvly mimie Nd All those dat have been by my side right from day one, dukka masoya na wanda na sani da wanda bansaniba , i love you all, Allah yabar zumunci